

# IKON RA'AYI KO ZABE

Dukan mu muna da zabin ababin da zamu yi kowace rana. Zamu yi kudurin inda zamu je, sutura da zamu sa, abin da zamu fadi, abinda zamu yi lokaci da hanya da zamu yi abu kaza da kaza da sauransu. Akashin gaskiya kowace rana tana hadde da ra'ayoyi daga safiya zuwa dare. Wandan su ra'ayoyi basu da kyau, kazalika wadansu daidai ne. Bugu da kari, ra'ayi mafi muhimmanci da zamu yi a duniya, shine ina ne zamu zauna har abada. Ko mu ki ko mu so, wata rana zamu fuskanci lahira. Wannan rayuwa na lokaci kadan ne, tana zama shiri ne zuwa madawami. Tambaya da ta rage shine inda zaka yi rayuwa a lahira in ka rabu da duniya nan. Wata-kila kana tare da Allah ko kuwa da Ibilis cikin kurama na wuta da makiyan Allah. A cikin duniya, Allah ya ba kowa da kowa zarafi ya ji bishara da kuma kudiri abin da zai yi da wa'azin.

Ko ka sani cewa kudiri da aniya ne zai nuna makomar ka alahira? Aniya ko kudiri tana da iko ainu. Allah ya ba kowa da kowa a duniya ikon zabe abin da zai faru da mu a duniya. Allah baya tilasta mu domin muyi wani abu. Wannan an nufi duk abin da ya faru da mu zaben mu ne da ayukan mu. Muna da iko mu bida abin da muke yi amma ba mu da iko akan sakamakon ra'ayin da mun zaba-suna nan din-din –din-din! Abin da ya kyautu mu gani cewa Allah baya tura mutane zuwa jaharnama, kai ne da zabi makomar ka na madawami! wutar jaharnama ba abin da an shirya domin mutum ba amma domin ibilis da masu bin ra'ayinsa domin su zabi kin kyautan Allah na madawamin rai sun kuma karasa da ibilis a jaharnama. Bai kyautu ka zauna hakka nan kawai ba ra'ayiba yanada muhimanci kayi zabe. Ko kaki yin zabe ma, zaka je jaharnama domin kasawa da mun gada ta wurin fadiwar Adamu wanda zunubi ne, kuma hakin zunubi mutuwa ne madawamiyar kayaswa (Romawa 3:23,6:23).

Yayin da yana cikin duniya, Yesu Kristi yace, “Barawo baya kanzo ba sai dai domin ya sata, ya kashe, ya hallakar: Amma na zo domin su sami rai, su kuma same shi cikake.” (Yahaya 10:10). Yesu ya dauke kamanin mutum, ya zo cikin duniya, ya sha wahala, ya mutu, an kuma bisne shi, ya yi nasara da ibilis ya tashi da rai cikin iko a rana ta uku domin ya sulhunta ka da Allah, domin ka sami raina har abada ya kuma

hada mu da shirin Allah domin rayauwar mu. Duk wannan yayi ne amadadin ka, ya dauke matsayin ka agaban Allah. Idan ka karba wannan yau zaka karbe rai na har abada wurin Allah. Ko zaka karba kamnar Allah ayau? Son ibilis shine domin ya hallakas da kai domin ka kasa gada rai da Allah ke bayaswa ta wurin Dansa Yesu Almasihu. Zabi domin ka zauna a mulkin ibilis ko kuma a yantar da kai, a kai ka mulkin Allah, ya rataya a wuyanka yanzu. Allah yana son ka gaje wannan madawamin rai, amma kafin haka ta faru, dole ne sai ka yadda domin ka karbi abin da Allah yayi ta wurin Dansa (Yesu Kristi- Cikaken hadaya) domin ka. Idan kana bukatan amsar wannan kira domin tuba, kayi wannan addua da bangaskiya daga cikin zuciyar ka. Ka yi shi yanzu, don Allah, kada ka yi jinkiri. Ka ce:

*"Ya Allah, na gode maka domin Dan ka Yesu Almasihu wanda ka bada shi ya mutu domin zunuban na, domin in gada madawamin rai maimaikon mutuwar madawami. Na yi furci Yesu Kristi ya zama ubangiji da mai cetona, na kuma bada gaikiya a cikin zuciyar na cewa ka tashe shi daga matattu domin ya kubutar da ni. Bisa ga maganar ka na yi furcin bangaskiya cewa, na sami ceto, ni sabon halitane, yanzu ina da rai na har abada. Ina rokon ka, ka cika ni da Ruhun mai Isarki ka kuma taimake ni in hadu da madawamiyar shirinka domin rayuwar ta. Na gode Uba, cikin sunar Yesu. Amin!"*

Na tayya ka murna! Maraba da zuma cikin iyalin Allah. Yanzu kai sabon hallita ne. yana da muhimmanci a gare ka ka sami littafi mai Tsarki, kana kuma karanta ta da yin addua a kowance rana ga Uban ka na sama, da zuwa ekklisiya da take koyas da Littafi mai Tsarki. Za ka iya tuntube mu, za muyi farin ciki mu gan mun taimake ka da yan takardu da zasu karfafa bangaskiyar ka cikin Kristi.

---

Domin ka karbi yan takardu a kyauta domin yin wa'azi da wadan su tambayoyi, ka tuntube a:

**LIFE COMMISSION MINISTRY**
+23470-32138935, +23480-59153304
P. O. Box 8272, Anglo-Jos, Plateau State, Nigeria
www.lifecommission.org / lifecommission@yahoo.com